# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na tara: Abokai da maƙiya ƙwallon ƙafar Afirka


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya tace: | Ludger Schadomsky da Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| John: | ɗan shekara 15 |
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| Anti Lily: | 'yar shekara 33 |
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| Insifeto: | ɗan shekara 40 |
| Metogba: | ɗan shekara 28 |
| 'Yar jarida: | 'yar shekara 25 |

**MAI GABATARWA:**
Masu sauraronmu, barkanmu da warhaka da kuma sake kasancewa da ku a cikin wani sabon shirinmu na “Ji Ka Karu” a kan wasan ƙwallon ƙafa a Afirka. A shirin da ya gabata, kun ji irin bayanin da ƙwararren ɗan wasan nan Metogba ya yi wa matasa ’yan wasa da ke gasa a ƙungiyarsa a kan barasa da ƙwayoyi a harkar wasannin ƙwallon ƙafa. An kama Honourable Gambo, sannan daga baya aka ba da belinsa, sannan an sallami Zakari kuma ya koma ƙungiyarshi a wajen da ake gudanar da gasar. Yau kuma za mu fara shirin ne daga gidan Honourable Gambo.

**Fitowa ta 1: A gidan Honourable Gambo**
John, Honourable Gambo

**HON. GAMBO:** John! Haba ɗana, ka saurare ni mana! Duk abin da na yi, na yi ne saboda kai. Har yanzu kai yaro ne, ba za ka gane ba.

**JOHN:** E, na ji ni yaro ne, amma ina fahimtar abubuwa. Abin da ka yi ba daidai ba ne. Baba, ka fa taɓa gaya min cewa, ana wasan ƙwallon ƙafa ne da ƙafafuwa da kai da ƙirji, ba da kuɗi ba da suke sa mutum yaudara da cin amana!

**HON. GAMBO:** Ina so ne ka zama ka fi kowa! Har yanzu kuma haka nake so. Yau ma zan je wurin wasan don in ba ka ƙwarin gwiwa.

**JOHN:** Mene?! Har za ka iya yarda jama’a su gan ka bayan abin kunya da ka yi?

**HON. GAMBO:** John, kwantar da hankalinka! Ni ɗan siyasa ne, kuma ina riƙe da ofishin siyasa. Jama’a na ƙaunata. Za a yi watsi da laifin da ake zargina da aikatawa. Dole maganata za a bi ba ta wani ɗan yaro ba, wanda ban da gantali ba abin da yake yi. Wa kake ganin kotu za ta yarda da shi?

**JOHN:** Haka ne? Shi ke nan, za kuwa ka sha mamaki. Za mu ga maganar wanda za a bi, tsakaninka da ’yan ƙungiyar da kuma tawa. Na ji shaidar da ta nuna cewa, kana da hannu dumu-dumu inda ka sa Shehu ya yi wannan fashin, kuma ya ɗora laifin a kan Zakari. A taƙaice dai za mu gani, maganarka za a bi ko kuwa ta jama’a. Ni na tafi filin wasa.

**HON. GAMBO:** Bari in kai ka mana.

**JOHN:** A’a, na gode, ba na so! Na so a ce na zama kamarka, na riƙa magana irin taka, ina yin yadda kake yi, har ma in riƙa wasa irin naka. Na ɗauka cewar kai masoyin wasan ƙwallon ƙafa ne, amma na gane cewa kai maƙiyin wasan ne. Ka ba ni kunya. Sai an jima!

**MAI GABATARWA:**
Idanun John sun yi ƙwalla a lokacin da ya wuce zuwa wurin wasan da za a yi. Mahaifinshi ya ba shi kunya matuƙa. A halin da ake ciki kuma, a gidan Anti, Safina da Anti Lily sun kusa kammala cin abincin rana.

**Fitowa ta 2: A gidan Anti Lily**

Safina, Anti Lily

**ANTI LILY:** Safina, kin ɗauka ina aiki a matsayin me?

**SAFINA:** To, za ki ga laifina ne, Anti Lily? Ba ƙaramar kunya na ji ba fa da kika faɗa min cewa kina aiki ne a gidan abinci. Amma ban gane ba. Me ya sa kike sa waɗannan ƙananan kayayyakin?

**ANTI LILY:** Saboda mai gidan abincin ya yi amana da cewa, ya kamata

masu ba da abinci su riƙa shiga mai kyau, kuma hakan na aiki. Alherin da nake samu ya fi albashin da yake ba ni a ƙarshen wata. Safina, ya kamata ki hanzarta saboda kada ki makara zuwa filin wasan.

**SAFINA:** Haka ne. Na yi matuƙar farin ciki. Anti Lily, na ji daɗi sosai da kika ce za ki zo kallon wasan. Da farko na ɗauka cewar ba ki ƙaunar wasan ƙwallon ƙafa, amma yanzu na ga kin zama mai ƙaunar wasan.

**ANTI LILY:** Ke kika sa ni ƙaunar wasan. Ke, Zakari, Metogba da sauran. Maza ki je ki shirya, bari ni kuma in kwashe kwanonin. Kina ta yin abubuwa da yawa.

**MAI GABATARWA:**
A yayin da Safina ta je ta shirya don ta tafi wajen wasan, a can caji-ofis kuwa, Zaks ne ya je ya ga tsohon babban abokinshi, wanda kuma yanzu ya zama maƙiyinshi, wato Shehu. Sai a biyo mu.

**Fitowa ta 3: A caji-ofis a garin Gabas**
Insifeto, Shehu, Zakari

**INSIFETO:** Yaro, kana da...

**ZAKARI:** …minti biyar, kuma a cikin nan, hakan yana nufin minti biyu da rabi ke nan.

**INSIFETO:** Lalle ba ka da mantuwa. Bari in ƙyale ku.

**ZAKARI:** Shehu, barka dai.

**SHEHU:** Me kake nema a wurina, Zaks? Ka zo ne ka yi min dariya

cikin nan?

**ZAKARI:** A'a, ba zan taɓa yin haka ba. Na zo ne dai in faɗa maka cewa yau ne za mu yi wannan babban wasan.

**SHEHU:** Na sani. Na ji duk ofisoshin da ke nan suna maganar. Wato yanzu ka zo ne kana neman goyon bayana, haka ne? Ina fata za a doke ku! Ina fatan a karya maka ƙafa, yadda ba za ka iya ƙara buga ƙwallo ba! Wasan ƙwallon ƙafa wasan banza ne. Dalilin da ya sa aka kawo ni nan ke nan.

**ZAKARI:** Ina tausaya maka, Shehu, gaskiya ina tausaya maka! Yanzu na gane cewa kai ba abokin gaskiya ba ne. Da ma can kana kishin iya ƙwallon da na yi, sannan bayan duk irin abubuwan da ka yi min, har yanzu kana jin haushina da nuna ƙiyayya. Ya kamata a ce ƙwallon ƙafa tana haɗa kawunan mutane ne, ta zama wata gada tsakanin gabas da yammaci, kudu da arewa, masu kuɗi da talakawa, baƙaƙe da farare, amma kai, kai da Honourable Gambo, kun kauce wa hanya. Sai wata rana, Shehu.

**SHEHU:** Ba za ka ci ba, Zaks! Ba za ka taɓa zama abin da kake so ka zama ba! Tun da dai kai ɗan titi ne, haka za ka ƙare rayuwarka kana gararamba a titi.

**INSIFETO:** Yi mana shiru!

**MAI GABATARWA:**
Wasan ƙwallon ƙafa a Afirka wani ɓangare ne na rayuwa. Wasu ma sun mai da shi tamkar addini. Ba mamaki shi ya sa filin wasan ya cika maƙil da 'yan kallo. Har shi kanshi shugaban ƙasa ya samu lokaci don ya halarci wasan. A yayin da Honourable Gambo yake kukkutsawa cikin jama'a don ya je wurin zaman manyan baƙi, sai ya hango wata fuska da ya sani.

**Fitowa ta 4: Wasan ƙwallon ƙafa a filin wasa**

Honourable Gambo, Anti Lily, Metogba, Zakari, ’Yar jarida

**HON. GAMBO:** Lily! Lily! Ke ce kuwa? Kai, Lily, gaskiya na daɗe ban gan ki ba. Shekarun na da yawa, ko? Shekaru nawa ke nan ma?

**ANTI LILY:** Mene ne bambancin a wurinka, Gambo? Me ya sa sai yanzu? Kana so ka san ko shekara nawa ne? Shekaru goma sha biyar ke nan. Shekaru goma sha biyar ina baƙin ciki da wahala.

**HON. GAMBO:** Lily, ki yi haƙuri, Lily! Lokacin yaro ne ni sakarai, mara wayo.

**ANTI LILY:** Dubi wanda yake magana. Ni lokacin shekaruna goma sha takwas ne kawai! Ka gudu, ka bar ni a lokacin da nake matuƙar buƙatarka.

**HON. GAMBO:** Lily, ba ki san yadda na yi nadamar yin wannan abin da na yi ba. Yanzu faɗa min, me ya faru da...kin gane...

**ANTI LILY:** Na yi abin da ya kamata in yi. Yanzu za a fara wasan, kuma ba na son wani abu ya wuce ni.

**METOGBA:** To fa a nan maganar take! Ko ta ware, ko ta waraye. Kun san cewa dai ’yan wasan ƙungiyar garin Gabas ƙwararrun ’yan wasa ne, amma ku tuna cewa, ƙwallon nan fa mulmulalliya ce. Ku tsai da hankalinku wuri ɗaya, ku yi wasa tare ban da son kai. Sannan kuma ko mun ci ko ba mu ci ba, mu dai mu ji daɗin wasan. Yauwa, kar in manta da wani abu guda ɗaya: masu hayar ’yan wasan nan suna cikin ’yan kallo. Maza, maza! *Go, go, go!*

**MAI GABATARWA:**

Ana watsa wasan kai tsaye ne a rediyo da talabijin saboda shugaban ƙasar ma ya zo kallo. Zakari na tunanin cewa mafarki yake yi, lokacin da ya ga irin yawan jama'ar da suka zo kallon wa? Shugaban ƙasar! Ya yi wata rantsuwa a zuciyarshi, kuma ba a daɗe ba ta zama gaskiya, a lokacin da muka fara bin wasan daga mai kawo mana labarin yadda wasan yake tafiya.

**'YAR JARIDA (a talabijin):** Muna cikin minti na talatin da ɗaya, kuma wasa ba ci in yanzu ka fara sauraronmu a wannan wasa tsakanin wata ƙaramar ƙungiya ta yara 'yan wasa, waɗanda suke cikin gasar zaɓen 'yan wasa da Metogba yake gudanarwa, da ƙungiyar ƙwallon ƙafa ta garin Gabas, zakarun nahiyar Afirka a shekarar bara. A halin da ake ciki dai, ƙaramar ƙungiyar ƙwallon ƙafan ta nuna ƙwazo na kare gidanta daga ci daga babban ƙungiyar kwallon ƙafan. A'a! Ga ƙwallo nan an bugo wa John, kuma... Wannan bugu daga John Gambo sai wanda ya gani, duk da cewa dai mai tsaron gidan ƙungiyar garin Gabas ya kaɓar da ita. Bugun kusurwa na farko, kuma abin mamaki, ƙananan 'yan wasa ne za su buga! Ga ƙwallo nan kuma, ga ta nan, ta tafi, me zai faru? *Goaaaaal!* Abin mamaki! Ɗan yaro Zakari ya jefa ta a ragar ƙungiyar garin Gabas, sun kasa gane abin da ya same su. Kwallo ta farko a ragar ƙungiyar garin Gabas. To fa, wasu masu goyon bayan ƙungiyar ƙwallon ƙafa ta garin Gabas ba su ji daɗin yadda alƙalin wasan ya yi musu ba. Wasu sun fara jefa kwalabe da duwatsu a filin wasan. Abubuwa sun fara lalacewa a wannan filin wasa. Jami'ai masu tsaron lafiyar shugaban ƙasar sun fice da shi daga filin. Shi ma alƙalin wasan ya kama hanyarshi ta fita daga filin. Wurin ya rincaɓe. A'a! Kowa na ta ƙoƙarin ganin cewa ya fice daga filin wasan a yayin da su kuma 'yan sanda suka fara jefa wa waɗanda suka ta da rigimar barkonon tsohuwa.

**METOGBA:** Zakari, ka ce wa kowa su fita daga filin nan! Kowa ya koma

ɗakin canza kaya!

**ZAKARI:** Metogba ya ce mu koma ɗakin canza kaya. Yanzu-yanzun nan da sauri!

**'YAR JARIDA:** Abin kunya ne a ce an daina wasan nan saboda kawai wasu 'yan tsiraru, waɗanda ba za su iya jurewa ba don an ci ƙungiyar da su ke so. Wani abu ɗaya da ya fito fili dai shi ne, ba wani abu da suke yi saboda ci gaban ƙwallon ƙafa a ƙasar nan. Mutane ne da ba sa ƙaunar wasan ƙwallon ƙafar. Yanzu ya rage ga Mr. Madu da ƙungiyar shirya wasan ƙwallon ƙafa ta ƙasar su ladabtar da waɗanda suka jawo wannan matsala. Yanzu bari mu koma ɗakinmu na watsa shirye-shirye.

**MAI GABATARWA:**

Da haka kuma muka kawo ƙarshen shirin na yau. Wai shin Anti Lily za ta iya barin filin wasan lafiya lau kuwa? Wane sirri ne take ɓoye wa Honourable Gambo har na tsawon shekaru goma sha biyar? Wa Metogba zai sanar a matsayin ɗan wasan da ya fi kowanne iya wasa, kuma ya ba shi kwanturagin da ya ce zai bayar? Wane ɗan wasa ne masu hayan 'yan wasa za su ɗauka, don su ba shi ɗaya kwanturagin? Duk waɗannan amsoshin tambayoyi za su zo muku ne a shiri na gaba. Sai a kasance da mu domin jin yadda za ta kaya. Kafin nan kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.